

Jagoran Jama'a

Littafin karatu a sauƙaƙe - Mataki na 4

Hausa

Zuwa ga malamai da iyaye:
Kafin a fara amfani da wannan tsarin koyon karatu, dole sai ɗalibi ya: • San amon sautukan haruffan Hausa; • Iya gane kalmomin da aka saba da su.

Jagoran Jama'a
Hausa Nigeria

Copyright © 2017, Enabling Writers Project - American University of Nigeria


http://creativecommons.org/licenses/by/4.0/
http://creativecommons.org/licenses/by/4.0/ An yarda ka yi amfani da wannan aikin ta wajen harkar kasuwanci. Kana iya ɗaukar aikin nan a yadda ya ke ko ka yi ƙari akai. Dole ne ka ajiye hakkin mallaka da kuma alaƙanta aiki ga marubuta, masu zayyana da sauran su. ISBN

Grace Malgwi Writing Trainer/Collection Editor
Prof Salisu Yakasai and Prof Lawan D Yalwa Hausa Language Consultants
Nas Yakubu Bloom Trainer
Story Writers Husaini Adamu; Adamu Babbikoi; Garba Mohammed Dantsoho; Jalauddeen Ibrahim Maradun; Yasalu Haruna; Muhammed Umar Deba; Idris Hamid; Ibrahim Baraya; Dahiru A Yelwa; Mansur Isah Buhari; Grace Malgwi
Illustration from International Illustration:The Art of Reading 3.0 Copyright: SIL International 2009



Jagoranci aiki ne na shugaba.
Jagoranci iri iri ne.
Akwai jagorancin iyali da na jama'a.
Duk jama'a ake jagoranta.

Maza suna jagoranci.
Mata suna jagoranci.
Ana samun jagora cikin manya.
Ana samun jagora cikin yara.





Jagorancin iyali a gida ake yi.
Iyali ya ƙunshi uba da uwa da 'ya'yansu.
Uba shi ne jagoran iyali.

Jagorancin jama'a shi ne na mutane duka.
Mutane a unguwa ko gari duka.
Jama'a suna bukatar jagora ko'ina.





Aikin jagora ne ya haɗa kan jama'a duka.
Aikin jagora ne ƙwato wa jama'a 'yanci.
Jagora yakan sa jama'a su bi doka.

Jama'a suna son jagora mai gaskiya.
Jama'a suna son jagora mai adalci.
Jama'a suna son jagora mai sonsu.
Jama'a suna son jagora mai mutunci.
Jama'a suna son jagora mai tausayi.



Jagora zai faɗawa jama'a gaskiya.
Jagora zai aikata gaskiya.
Jagora zai sa jama'a su yi gaskiya.
Jagora zai so mai gaskiya.
Kowa yana son jagora mai gaskiya.





Jagoranci aiki ne na mai hakuri.
Jagoranci aiki ne na mai tunani.
Jagoranci aiki ne na taimakon jama'a.
Jagoranci aiki ne na mai ilmi.

ALL CHILDREN READING: A GRAND CHALLENGE FOR DEVELOPMENT

USAID FROM THE AMERICAN PEOPLE

World Vision

Australian Aid

GLOBAL READING NETWORK